# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Almara a Afirka domin al’adu da zaman lafiya:
## Bari na ba ku labari
## Na ɗaya: Badaƙalar Kwaɗo


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Ibrahima Ndiaye |
| Waɗanda suka tace: | Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |


**’Yan wasa:**

Mai ba da labari

Kwaɗo

Tsaka

Hawainiya

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, yaushe rabonku da sauraron tatsuniya? Ba mamaki jiya ma kun saurara, ko a makon da ya shige, ko kuma tun bara. To a wannan karon, cikin sabon shirinmu na “Ji Ka Karu” mai taken “Bari na ba ku labari”, za mu leƙa ne taskar irin hikayoyin nan na Afrika masu cike da darussan da suke koya zamantakewa tsakanin al’umma.

Hikayoyi sun ƙunshi al’amura na zahiri, kuma a wani lokacin ma, sukan zama mubuɗin ilimi ga mutum. Kamar yadda kowa ya sani ne cewa duk al’ummar da mutanenta ke zaune lafiya, to ba shakka za ta ci gaba. Don haka, hikayoyin da za mu kawo sun shafi rikice-rikice da kuma yadda ake sasanta su. Misali, ta yaya mutum zai iya warware wata matsala mai sarƙaƙiya? Yaya mutum zai yi a wani yanayi da ya samu kansa na rashin gaskiya, ko hassada ko son rai? A kowanne daga cikin labaran da za mu kawo muku, akwai wani abu mai amfani da zai taimaka wa mutum a rayuwarsa, ko ba daɗe ko ba jima.

Don haka, sai ku biyo mu, ku saurari wannan labari namu na farko da kyau, don ku ji dalilin da ya sa Kwaɗo yake rayuwa a wuri mara tsafta. Taken shiri na yau dai “Badaƙalar Kwaɗo”. Labari ne a kan aminci da yarda da kuma cin amana.

MAI BA DA LABARI:

> Can a zamanin da, Kwaɗo aminin Tsaka ne. Sun kasance abokan juna, kuma sun amince da juna matuƙar amincewa. Wata rana, lokacin kuwa ana tsananin zafi, ga iska mai ƙarfi na kaɗawa, sai Kwaɗo ya kai wa mutuniyarsa Tsaka ziyarar ba-zata. A lokacin ita kuma Tsakar tana hutawa a gindin wata inuwar bishiyar kuka.

KWAƊO:

> “Salama alaikum, ƙanwata! In ce ko dai lafiya?”

MAI BA DA LABARI:

> Kwaɗo ya tambaye ta cikin girmamawa.

TSAKA:

“Lafiya, yayana, zafi nan ne kawai yake damuna. Sai kuma cikina da yake ta kiran ciroma.”

MAI BA DA LABARI:

Tsaka ta amsa masa, wadda da ganinta za ka san cewa a jigace take.

KWAƊO:

“To me zai hana ki biyo ni mu je mu sha mangwaro.”

MAI BA DA LABARI:

Tsaka dai ba ta wuce tayi ba, saboda halin da take ciki. Don haka, sai ta tashi suka rankaya. Haka suka kama hanya suna tafe suna ta barkwancinsu suna dariya, sai kwatsam suka hangi wata gona cike da bishiyoyin mangwaro nunannnu, abin gwanin ban sha’awa.

TSAKA:

“To fa, babban yaya, yau fa za mu sha shagalinmu. Ai ganin waɗannan mangwarorin ya sa har yawuna ya tsinke. Ka ga, mu yi maza mu yi abin da za mu yi kafin mai gonar nan ya zo. Ni zan hau bishiyar in tsinko, kai kuma ka tsaya kana dubawa. Da zarar ka ji wani abu, sai ka yi gyaran murya.”

MAI BA DA LABARI:

Tsaka na gama wannan bayani, sai ta yi ɗaraf ta haye bishiyar mangwaro, ta fara sharɓa ba ji ba gani, ta bar abokin tafiyar tata yana gadi.

TSAKA:

“Mhmm…mhmm…mhmm.”

MAI BA DA LABARI:

Haka dai ta yi ta yi tana ta zazzare idanu. Saura kaɗan wani ƙwallo daga cikin waɗanda ta shanye ya sauka a kan Kwaɗo, wanda hakan ya sa ya kasa daurewa.

KWAƊO:

"Haba ƙanwata, yaya kike nema ki manta da ni ne? Na tabbatar sha kike ta yi, bayan kuma ni na fara ganinsu. Don Allah jefo mini mana!"

MAI BA DA LABARI:

Haka dai Kwaɗo ya ci gaba da yi wa Tsaka magiya, har wannan magiyar ta fusata ta.

TSAKA:

"Ka ga, ni dai na yi min magiya sai ka ce almajiri! Ni fa mitar nan taka ta ishe ni! Wato so kake na ƙware ko? Ni gaskiya zan daina yawo da kai."

MAI BA DA LABARI:

Tsaka na gama faɗar wannan magana, sai kawai ta juya ta ci gaba da sharɓar mangwaronta. Kwaɗo da ya fahimci cewa abin son rai ne kawai ƙarara, sai kawai ya ga gara ma ya yi shiru kawai.
Daga nan sai wata dabara ta faɗo wa Kwaɗo. Sai ya hura wuta ganga-ganga a gindin bishiyar mangwaron nan. Nan da nan sai hayaƙi ya turnuƙe ya yi sama har ya sa Tsaka ta fara shaƙewa.

TSAKA:

"Kai, me ya same ka ne? Ba ka jin zafi ne, ko an gaya maka ana gasa mangwaro ne? Wannan ai hauka ne!"

MAI BA DA LABARI:

Kwaɗo ya yi banza da ita. Nan da nan Tsaka sai ta fara tari ba ji ba gani. Sai ta ji kamar ma ta amayar da kayan cikinta.
Can bayan wani lokaci sai Kwaɗo ya amsa:

KWAƊO:

“Yi haƙuri, kin ji ƙanwata. Wallahi sanyi ne ya dame ni, ji nake kamar na shiɗe. Ni kuma matsalata ita ce da sanyi ya kama ni sai muryata ta shaƙe.”

MAI BA DA LABARI:

Ai Kwaɗo bai ƙara cewa kome ba, sai kawai ya yi ta hura wutar nan har sai da Tsaka ta sallamo cikin garwashi. Duk da cewa Tsaka ta tsira da ranta, amma har yau in ka gan ta za ka ga jikinta akwai ɗishi-ɗishin ƙuna.

Daga nan sai Tsaka ta je ta yi ta bazawa a cikin gari cewa, wai wannan shashan Kwaɗon, yana ƙyashin ganin ta iya hawa bishiya, sai kawai ya watsa mata garwashi yayin da take hutawa.

Nan da nan sai aka haɗa gangamin neman Kwaɗo don a koya masa hankali. Take, sai sauran dabbobi suka fita neman Kwaɗo cikin fushi. Shi kuwa Kwaɗo sai ya ɓuya a gidan Hawainiya, wanda wani babban boka ne da kowa ke jin tsoronshi. Sai Kwaɗo ya faɗa mata gaskiyar abin da ya faru, sannan ya roƙe shi:

KWAƊO:

“Don Allah, Hawainiya, ina roƙonka ka taimake ni! Ba zan iya kare kaina ba, ka san ba ni da wani ƙarfi!”

MAI BA DA LABARI:

Hawainiya sai ya tausaya masa ya kuma haɗa masa wani magani, sannan ya ce masa:

HAWAINIYA:

“Wannan maganin zai sa ka ji wani irin ƙarfi ya zo maka. Ka sha, amma bisa sharaɗin ba za ka cutar da kowa ba!”

KWAƊO:

"Na yi maka wannan alƙawarin ƙwarai da gaske. Kada ka ji kome."

MAI BA DA LABARI:

Wannan shi ne alƙawarin da Kwaɗo ya yi. To, ba tare da wani ɓata lokaci ba sai Kwaɗo ya shanye maganin nan, suka kuma yi sallama da Hawainiya.
Kwaɗo sai fa ya dinga kuri, yake kuma neman ya mallake sauran dabbobin. Sai ya tara su gaba ɗayansu amma ban da Hawainiya, ya ce:

KWAƊO:

"Daga yanzu ni ne sarkinku gaba ɗayanku, kuma duk wanda yake da ja, to ya fito mu gwada 'yar ƙashi!"

MAI BA DA LABARI:

Duk wurin sai kowa ya ji shi kawai, tun ba ma Tsaka ba da abin ya ba wa dariya. Nan da nan sai Kwaɗo ya yi tsalle a dira a kanta, ya maƙare ta har ya kusa kashe ta. Wannan abin ya ba sauran dabbobin mamaki. Ai fa ganin haka sai wani Zomo ɗan duniya ya yi wata dabara, amma kafin ka ce kwabo, sai ga shi an yi sama da shi an jefa shi a wata gona. Kai har Karakanda da Zaki ma sai da suka sallama wa Kwaɗo.
Wannan ya harzuƙa Giwa wadda ya sa ta yi wata irin kururuwa, ta kai wa Kwaɗo bara. Kowa sai ya yi tsit. Nan fa Kwaɗo ya yi wuf ya shige cikin kunnen Giwa, ya dinga kukan kwaɗi, sai da Giwa ta ji kamar haukacewa za ta yi. Ta yi ta fafutukar ƙwaƙwalo shi daga kunnenta da wannan dogon hancin nata, amma ina! Ai fa sai kawai ta kama zagayawa a rikice. Saboda irin yadda ta dinga buga ƙafarta, sai da ƙasa ta dinga rawa, har Hawainiya ya faɗo daga bishiyar da yake kwance nan kusa da su.
Nan fa sai Hawainiya ya ce bari ya bincika ya ga me ya jawo wannan hargowa. Ganin dukkan dabbobi sun taru sun yi tsuru-tsuru, ga Giwa a tsakiya, sai ya ba shi mamaki. Da ya saurari abin da sauran

dabbobin suka ce, sai nan da nan hankalin Hawainiya ya dugunzuma:

HAWAINIYA:

"Kai Kwaɗo! Ka saɓa alƙawarin da ka ɗauka! Horon da zan yi maka shi ne, za ka daina jin wannan ƙarfin da na ba ka, sannan kuma daga yau makomarka ita ce, za ka ci gaba da rayuwa a wuri mafi muni!"

MAI BA DA LABARI:

Ba tare da wani ɓata lokaci ba, sai Hawainiya ya sa dogon harshen nan nashi ya naɗe Kwaɗo ya yi sama da shi facal! Sai ga Kwaɗo ya yi wanwar a taɓo cikin wani ɗan kududdufi, inda har yau a nan yake rayuwa cikin ƙasƙanci.

Wannan ita ce hikayar tamu ta yau. Duk wanda ya yi amfani da darussan da ke cikinta, to shi ya rabauta.

MAI GABATARWA:

Wannan shi ne ƙarshen hikayarmu mai suna "Badaƙalar Kwaɗo". Wanda ya rubuta ta shi ne Ibrahim Ndiaye, marubucin labaran nan ɗan ƙasar Senegal. Yaya kuka ji labarin dai? Kun taɓa samun kanku a wani yanayi da kuka ji ba wanda ya fi ku? Ku sanar mana ta adireshinmu na imel, wato lbe@dw-world.de, ko kuma ku bayyana mana ra'ayinku ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe. Sai a wani sabon shirin idan Allah ya kai mu.